(١)

## GINSHIƘAN TSARO A RAYUWAR ZAMANTAKEWA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Su ne waɗanda suka yi imani, ba kuma su cakuɗa imanin nasu da zalunci ba, lallai waɗannan su ne suke da cikakken tsaro, su ne kuma shiryayyu)** [al-An’ami: 82], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai ni’imar samun tsaro da aminci tana cikin manyan ni’imomin da Allah mai girma da buwaya yake yi wa bayinsa, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Ku yi mamakin irin yadda na sauƙaƙe wa Ƙuraishãwã wurin. Yin balaguronsu a lokacin ɗãri zuwa ƙasar Yaman, da kuma balaguron lokacin rãni zuwa garin Sham cikin kwanciyar hankali da tsaro; saboda kasuwanci da neman arziki. Saboda haka, ya kamata su tsarkake ibada ga Ubangijin wannan ɗaki da ya ba su lamunin waɗannan tafiye-tafiye biyu a duk shekara. Wanda shi ne ya ciyar da su a lokacin da suke cikin yunwa; domin suna rayuwa ne a wuri faƙo, ya kuma tabbatar masu da tsaro, a daidai lokacin da ake wa maƙwabtansu ɗauki ɗai-ɗai)** [Ƙuraish- 1 -4], haka ma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ashe ba mu ba su cikakken iko da faɗa a ji akan Harami mai cike da tsaro, ta yanda ake kawo masu dukan kayayyakin marmari a matsayin arziki daga gare mu ba?! Sai dai mafi yawansu ba su sani ba)**

[al- Ƙasasi: 57], haka ma Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Ashe ba su ga cewa mu sanya Harami ya zama mai cikakken tsaro, sa'ilin da ake yi wa mutanen garuruwan da suke gefensa ɗauki ɗaiɗai ba?! Yanzu da ƙarya za su yi imani, su kuma kafirce wa ni'imar Allah)** [al- Ankabut: 67], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya wayi gari cikin aminci yana cikin iyalansa, ga lafiya a jikinsa, yana kuma da abincin da zai ci a ranar daidai yake da wanda aka ba shi duniya ɗungurungun).**

Babu shakka kan cewa shi tsaro, aiki ne da ɗaukacin al'umma da 'yan ƙasa suke tarayya da juna wajen samar da shi, saboda babu yanda za a yi mutum ya iya samar wa kansa, ko iyalansa da tsaro ba tare da la'akari da tsaron ɗaukacin al'umma ba, lallai mutane a garuruwansu da ƙasashensu sun yi kama da fasinjojin jirgin ruwa, waɗanda babu yanda za a yi wasu su tsira ba tare da saura ba, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Misalin mutumin da yake tsaye akan iyakokin Allah, da wanda ya auka cikinsu, kaman mutanen da suka shiga cikin jirgin ruwa ne, wasu suka samu wuri a sama, wasu kuma suka samu a ƙasa, sai ya zamana idan na ƙasan suna buƙatar ruwa sai sun biyo ta wurin waɗanda suke samansu, sai suka ce: da za mu huda wani wuri a inda muke, ta yanda ba za mu dami waɗanda suke samanmu ba, idan na saman suka barsu suka aikata abin da suka yi nufi, dukansu za su halaka, idan suka hana su, sai su tsira, sai dukansu ma su tsira)**

Lallai shi wannan tsaro na dukan al'umma yana da ginshiƙai da shika- shikai, a cikinsu akwai: Ƙarfafa sashen imani wanda shi ne yake samar da natsuwa a cikin rayuwar zamantekwar al'umma, ya kuma kare ta daga cutar wuce gona da iri, da ta saɓa

lamba a wajen tunani, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Su ne waɗanda suka yi imani, zukatansu kuma suka sami natsuwa saboda ambaton Allah, lallai da ma can da ambaton Allah ne zukata suke samun natsuwa)** [ar- Ra'ad: 28], lallai imani da Allah mai girma da buwaya shi ne yake samar da tsaro a cikin gida tsakan ɗaukacin al'umma, wanda kuma hakan yake haifar da tsaro na gaba ɗayan al'umma.

Haka ma a ciki akwai: Sashen tattali, da tsumi da tanadi, wanda ya ginu akan aiki tuƙuru, da kuma sana'anta kayayyaki da kuma kyautata su; saboda haka ne addininmu mai daraja ya kwaɗaitar da mutane game da muhimmancin aiki, da kuma yinsa da kyau, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Ka kuma ce masu: ku yi aiki, da sannu Allah zai ga ayyukanku, Manzonsa da sauran muminai ma za su gani)** [at- Tauba: 105], haka ma mabuwayin sarki yana cewa: **(Ka kyautata irin yanda Allah ya kyautata maka, kada ka nemi aikata ɓarna a bayan ƙasa, lallai Allah ba ya son maɓarnata)** [al- Ƙasasi: 77], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah yana son idan wani daga cikinku zai yi aiki, to ya yi aikin da kyau),** da haka sai tsaro ya samu, al'umma ta sami kwanciyar hankali.

Haka ma a cikinsu akwai: Kafa da ƙarfafa kyawawan ɗabi'un taimaka wa marasa shi, da kuma sanya tausayi tsakanin 'yan ƙasa ɗaya da junansu, lallai addininmu mai daraja ya bai wa wannan sashe muhimmanci na musamman; saboda haka ne aka farlanta zakka, aka kuma kwaɗaitar da yin sadaka, aka shar'anta bayar da waƙafi, aka kuma ƙarfafi mutane akansa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai halin waɗanda suke bayar da dukiyoyinsu wajen yi wa Allah biyayya da hanyoyin alhairi, suka kuma**

**sami ladan Allah akan haka, ladan kuma ninkin-ba-ninkin, ya yi kama da halin mutumin da ya shuka iri ne a ƙasa mani'imciya, irin kuma ya tsirar da 'yar ƙaramar bishiya mai zangarniyoyi bakwai, cikin kowace zangarniya akwai ƙwaya ɗari. Wannan sura ce ta yawan abin da Allah zai ba shi na sakamakon ciyarwa a duniya, Allah yana ninninka haka ga wanda ya ga dama, domin shi mai yalwan falala ne, yana kuma da cikakken sanin wanda ya cancanta da wanda bai cancanta ba)** [al- Baƙra: 261], haka ma Allah mabuwayin sarki yana cewa: **(Shi kuwa abin da kuke bayarwa na taimakon waninku, amfaninsa ku ne zai dawo wa, Allah zai ba ku lada akai, wannan fa idan ba ku nufi komai ba wajen ciyarwar sai neman yardar Allah kenan, duk wani abu na alhairi da za ku ciyar ta wannan hanyar zai dawo zuwa gare ku, ladansa zai sadu da ku a cike ba tare da an tauye maku ba)** [al- Baƙra: 272], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: (**Duk wanda ya yaye wa Mumini wani baƙin ciki na duniya, Allah zai yaye masa baƙin ciki daga cikin baƙin cikin ranar alƙiyama, duk wanda ya sauƙaƙa wa mara shi, Allah zai sauƙaƙa masa a duniya da lahira, duk wanda ya suturta Musulmi Allah zai suturta shi a duniya da lahira, Allah yana taimakon bawansa matuƙar bawan yana taimakon ɗan uwansa)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda yake da abin hawa bayan abin hawansa, to ya bayar da shi ga wanda ba shi da abin hawa, haka ma duk wanda yake da guzuri da ya wuce buƙatarsa, to ya taimaka wa wanda ba shi da guzuri)**, har sai da muka zaci cewa duk abin da ya fi ƙarfin buƙatunmu ba haƙƙinmu ba ne.

A cikin muhimman ginshiƙai da shika- shikan tsaro a cikin rayuwar zamantakewa ta al'umma akwai tabbatar da daidaito tsakanin mutane, lallai mutane daidai suke da juna kaman haƙoran matsefi, wayayyiyar al'umma da take rayuwa cikin tsaro da aminci ba ta bambance tsakanin 'ya'yanta akan bambancin harshe ko na launin fata, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ya ku mutane, ku sani Ubangijinku ɗaya ne, babanku ma ɗaya ne, ku sani Balarabe ba shi da wani fifiko akan wanda ba Balarabe ba, haka ma wanda ba Balarabe ba ba shi da wani fifiko akan Balarabe, farin mutum ba shi da fifiko akan baƙin mutum, haka ma baƙin mutum ba shi da wani fifiko akan farin mutum sai da tsoron Allah..)**, ba a samun bambanci, ko fifiko tsakanin 'yan ƙasa sai gwargwadon ƙwarewa da baiwa, da kuma kuma irin yanda kowa yake gabatar da ƙoƙarin da zai taimaki al'umma.

****

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Babu shakka samar da kyakkyawan yanayi yana cikin muhimman ginshiƙai da shika- shikan tsaro da aminci a rayuwar zamantakewar al'umma, ta hanya kyautata samar da yanayi mai kyau, da kiyaye shi ga barin dukan cutuwa ko hatsari, Allah mai girma da buwaya yana cewa: (**Shi ne ya halicce ku da ƙasa, ya kuma nemi da ku raya ƙasar..)** [Hudu: 61], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Musulmi ba**

**zai taɓa dasa wata bishiya, mutum ya ci daga ciki,** ko **wata dabba, ko wani tsuntsu, face hakan ya zamo masa sadaka a ranar alƙiyama)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Imani ya kasu kaso saba'in da wani abu –ko sittin da wani abu-, mafi girmansa shi ne faɗin *"La'ilaha illalLah"*, mafi ƙanƙantarsa kuma kawar da abu mai cutarwa daga hanya, kunya ma kaso ne daga cikin imani).**

Lallai muna matuƙar buƙatar haɗa ƙarfi da ƙarfe, saboda mu samar da cikakken tsaro da aminci a rayuwar zamantakewa, da kuma kiyaye ta, ta hanyar haɗa ayyukan ɗaukacin ma'aikatun gwamnati, soja, da 'yan sanda, da sashen shari'a, da gida, da makaranta, da hukumomin addini, da na al'adu da sauran al'umma; saboda ɗaukacin ƙoƙari da ayyukan 'yan ƙasa su sami haɗuwa akan manufa guda ɗaya a tare.

**Ya Allah Ubangiji, muna roƙon ka dawwamar mana da ni'imomin, ka dawwamar wa ƙasarmu mai daraja da ni'imar tsaro da aminci da kwanciyar hankali, da ma sauran ƙasashen duniya.**